# TARBIYYAR 'YA'YA DAGA NEMAN AURE HAR ZUWA BALAGARSU



Daga

Shehu Mansur Dala

**TARBIYYAR 'YA'YA DAGA NEMAN AURE HAR**

**ZUWA BALAGARSU**

**GABATARWA**

Bismallahi wassalatu wassalamu ala rasulullahi wa alihi wa sahabihi wa sallam.

Babban burin kowane miji da mata bayan an yi aure shi ne samun ‘ya’ya managarta waɗanda za su zama farin ciki ga Iyaylinsu da duniya da lahira.

Amma fa ya wajaba a sani cewa sai fa an yi tarbiyya Sannan ake samun ‘ya’ya na gari wato dai yanzu nauyi ya ƙaru a kan ango da amarya yanzu kun zama umma da baba. A kan haka na rubuta wannan taƙaitacciyar maƙalar domin sanin makamar aikin tarbiyya.

Da farko ya kamata uwa da uba su sani cewa aikin tarbiyya wajibi ne kamar yadda salla da azumi da sauran ibadu suke wajibi

Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ce: "Kowane ɗaya daga cikinku mai kiwo ne kuma za a tambaye shi kan abinda aka ba shi kiwo. Za a tambayi shugaba a kan talakawansa, za a tambayi maigida a kan iyalinsa, za a tambayı uwárgida a kan mutan gidanta

**(Bukhari da Muslim).**

Sayyidina Ali (Radiyallahu Anhu) ya ce: ya fassara faɗin Allah Ta'ala: Ya ku waɗanda kuka yi Imani ku kiyaye kawunanku da na iyalanku daga wuta. (Surat Tahrim: 6) da cewa: "Ku koyar da kawunanku da iyalanku, abubuwan alhairi, Ku koyar da su ku yi musu tarbiyya.”

Ibnul Kayyim (Radiyallahu Anhu) ya ce: "wani malami ya ce: * Ranar Ƙiyama sai Allah Ta' ala ya fara tambayar uba a kan tarbiyyar ɗansa, kafin ya tambayı ɗa a kan biyayya ga ubansa. Saboda kamar yadda uba yake da haƙƙi a kan ɗansa, haka shi ma ɗan yake da haƙƙi a kan ubansa.

**(Tuhfatul Maudud)**

Saboda waɗannan dalılai na rubuta wannan yar muƙala a matsayin kayan barka ga uwa da uba musamman sababbin shigowa. Allah ya raya 'ya yanmu. ya yi musu Albarka.

Ya kamata mai karatu ya san cewa asalin wannan littafi maƙala ce da na rubuta domin yin bita ga Samari da magidanta da 'yan mata da matan aure mai taken: Kimiyya da fasahar zaman aure. Na gabatar da wannan bita a wurare da makarantu da dama, kuma wannan maƙalar ita ce ta goma sha biyu kuma ta ƙarshe a jerin maƙalolin wannan bitar.

Ganin muhimmacin abinda ta ƙunsa malama Hafsa Abubakar Shugabar makarantar Raudatul Islam da ita da malaman makarantar suka ga ya kamata na sake yin jagorancin nazarinta domin su ɗauki nauyin buga ta saboda amfaninta ya yaɗu ga ɗimbin al'umma.

Allah ya sakawa malama da alhairi da sauran malamai da jagororin makarantar. Amin.

Shehu Mansur Dala

12/4/1441Al 09/12/2019

**AIKIN UBA**

Babban nauyi a wajen tarbiyya yana kan uba, kuma duk Kulawar uwa in uba bai yi nasa aikin ba to sai an samu matsala a tarbiyyar ‘ya’ya.

A dunƙule ga wasu daga Cikin nauye-nauye da suke kan uba,

1. Zaɓen mace managarciya mai addini.
2. Kaucewa saɓon Allah a lokacin neman auren,
3. Kaucewa saɓon Allah a lokacin biki.
4. Kula da haƙƙoƙin da matarsa take da su a kansa.
5. Kula da ladaban ma'amalar aure a ranar farko,
6. Cikakkiyar kulawa da matar a lokacin da take da ciki. kula da lafiyarta da tausaya mata da taimaka mata da kwantar mata da hankali. Haka a lokacin da take naƙuda, da lokacin da ta haihu.
7. Nuna farin ciki da godiya ga Allah kan duk abinda ta Haifa mace ko namiji
8. Cikakkiyar kulawa da lafiyarta da faranta mata da taimakonta da ciyar da ita a lokacin da take shayarwa.
9. Yin hidinmomin jariri waɗanda suka haɗa da sa masa suna mai kyau. yi masa aski, yi masa kaciya, yanka masa ragon suna, da al'adu masu kyau na nuna farin ciki waɗanda ba su ci karo da shari'a ba.
10. Daga nan kuma sai a duƙufa wajen tarbiyyar jiki. hankali, tunani, ilimi, zamantakewa, ƙwaƙwalwa, siyasa da sauransu tun daga wannan lokaci har zuwa balagar ɗa namiji da aurar da 'ya mace kamar yadda Za’a a yi bayani a nan gaba da kuma sauran maƙaloli da za su zo in sha Allahu.

## AIKIN UWA

Ita ma uwa tana da nata ayyukan masu yawa da muhimmanci waɗanda in ta kula da su za a samu 'ya' ya na gari in sha Allahu, daga cikinsu akwai:

1. Zaɓen muji na gari ta zaɓa ko a zaɓa mata.
2. Kaucewa saɓon Allah 1a ala a lokacin neman aure da lokacin biki, da kula da haƙƙoƙin da miji yake da su a kanta
3. A yayin da kika samu ciki ki yawaita addu ar Allah ya tsare ki da abinda yake cikinki daga sharrin shaiɗanu.
4. Ki kula da bin Allah Ta'ala da kaucewa saɓa masa.
5. Ki kula da cin abinci mai gina jiki da ƙara lafiya. musamman irin abincin da likiitoci suke bai wa mai ciki shawara ta rinƙa ci ki rinƙa bin shawarwarin lokitoci na kula da lafiya.
6. Ki yi ƙoƙarın iya yinki. wajen kaucewa ɓacin rai da janyo wa kai fitina. da tashin hankali tsakaninki da mijinki ko abokan zamanki.
7. Ki guji shan tsami da ɗaci da magunguna barkatai .ba tare da umamin likita ba.
8. Zubar da ciki haramun ne ahir ɗinki!.
9. Ki kula da tsaftar jikinki da mahallinki da abinciki
10. Ki rinƙa daurewa kina motsawa kina yin aikace-aikacen gida kada ki lafke ki daina komai sai kwanciya.
11. Ki guji shan taba da sauran shaye-shayen kayan maye saboda illarsu da cutarsu har abinda yake cikinki yake shafa.
12. Da zarar kin ji ba daidai ba a jikinki ki tunutuɓi likita.
13. Ki guji yawan yin "Scanning yana da illa. Sai da umarnin ƙwararren likita.
14. Kada ki mayar da ciki da haihuwa wata hanyar gallazawa miji da cusguna masa da ɗora masa laluron da tsarabe-tsarabe na ba gaira ba dalili, ta yadda samun ciki zai zamo wani abin ɓacin rai da damuwa ga mijinki.
15. Ki tabbatar kuna bin shawarwarin likitoci wajen shanayar da jariri Ki ara kula da cin abinci mai gina jiki a lokacin da kike shayarwa.
16. Ki kula da lafiyar jaririnki, ki yi ta yi masa addu a.
17. Ki kula da ƙa'idodin tarbiyya tun daga goyon ciki nar zuwa girma da balagar 'ya yanki.

18. Tarbiyya aiki ne na uwa da uba duk wani wanda zai shigo tamaka musu kawai zai yi. Saboda haka ku ɗaura ɗamara ku dage ku nemi taimakon allah kada ku yi sakaci. A kula a yi hattara.

## HAƘƘOKIN ƘANANAN YARA

## A MUSULUNCI

Sarakan karaɗi da surutun duniya suna ta murgina kai suna Jin cewa wai su ne suka tabbatar da haƙƙoƙin kananan yara. Ba su sani ba ko sun sani sun take cewa tuni addinin Musulunci ya yi gaba wajen kafa dokoki da tabbatar da aiki da su don kare haƙƙoƙin ƙananan yara. A nan a taƙaice zan kawo su kafin in sami wata damar ta yin bayani filla filla in sha Allah.

1. Ƙananan yara suna da haƙƙin a zaɓa musu uwa da uba na gari
2. Kula da ladaban mu'amala da iyali, domin a samu ya'ya masu albarka.
3. Wajibi ne a kula sosai da mai ciki, ita ma ta kula da kanta.
4. Ba a yi wa mai ciki haddi saboda abinda take ɗauke da shi.
5. Wajibi ne a ciyar da mai ciki a kula da lafiyarta koda kuwa an sake ta ne, haka kuma a lokacin da take shayarwa.
6. An halattawa mai ciki da mai shayarwa su sha azumi idan suna tsoron ɗansu zai shiga wani yanayi.
7. Zubar da ciki haramun ne.
8. An haramta yin ta'addanci ga jaririn da yake ciki. Wato harmun e a daki mai ciki ko a firgita tata yadda ɗan cikin zai samu wata lalura ko ma ya mutu.
9. Ba a raba gado in dai akwai ciki, saboda shi ma yana da gado. Sai a bari sai an haihu an ga abinda aka samu Sannan a raba a fitar masa da rabonsa a ajiye masa har Sai ya girma.
10. Ana yi wa ɓari da halittarsa ta cika komai da ake yiwa gawar babban mutum wato a yi masa wanka a sa masa likkafani a yi masa salla a binne shi.
11. An hana dakatar da haihuwa ba tare da wata lalura ba.
12. Yara suna da haƙƙin a sa musu sunaye na gari, kyawawa.
13. Suna da haƙƙm a yi musu yanka ranar suna.
14. Suna da haƙƙin a yi musu aski.

15. Suna da haƙƙin a yi musu kaciya (maza)

16. Suna da haƙƙin a kula da lafiyarsu, tun suna ciki har su girma.

17. Suna da haƙƙin a kula da cikakkiyar tarbiyyarsu tun suna ciki har zuwa gimansu da balagarsu.

## HUKUNCE-HUKUNCEN ƘANANAN YARA

Akwai hukunce-hukunce da dama da suka shafi ƙananan yara masu yawa waɗanda ya wajaba ga iyaye su san su tun kafin yin aure da samun cikin yaron.

A bayanin da ya gabata na ɗan taɓo wasu daga cikin waɗannan hukunce-hukunce, ɗari a kansu shi ne

1) Ya halatta a huda kunnen mace saboda ado duk da cewa za ta ji zafi.

2) An fi so a yi wa namiji kaciya tun kafin-ya fara jin kunyar tsiraici, waɗansu malanman suna ganin ya kanata a yi wa yaro kaciya ranar bakwai.

3) Kaciyar mata ba wajibi ba ce, in akwai matsala ya kamata a bar ta.

4) An yi sauƙi a yayyafa ruwa a kan fitsarin ƙaramin yaro da ba a yaye shi ba, amma na jaririya sai an wanke.

## HUKUNCE-HUKUNCEN RAINO

Idan aka samu saɓani tsakanin miji da mata har ya kai ga rabuwa ga kuma ƙananan yara to akwai hukunce-hukunce na musamman da Suka haɗa da:

1- Lallai ne uwa ta ɗauki rainon ya'ya in babu wacce za ta yi sai ita.

2- Amma idan akwai wata kuma 'ya' yan ba za su cutu ba in an raba su da uwarsu, to ba za a tilasta mata ta raine suba.

3- Bai halatta ba uba ya ƙwace ɗa daga hannun uwa ba, ba tare da wani dalili na shari'a ba. Yin aure ko rashin lafiya ko rashin tarbiyya yana daga Cikin waɗannan dalilai.

4- Uwa ita tafi cancantar ta yi raino, sai kaka, ta ɓangaren uwa, sai innar ɗan, sai kaka ta ɓangaren uba, sai yar uwa, sai gwaggon ɗa, sai 'yar ɗa, sa mai riƙo sai asibi.

5- Lallai ne mai raino ta kasance musulma, baliga, ma hankali, mara aure, wacce ta cancanci ta yi tarbiyya. ya managarciya mai adalci.

6- Ya wajaba uba ya biya uwa ladan raino in ba tare suke ba.

7- Lokacin raino yana ƙarewa daga balagar namiji da aurar da mace.

Ina ba da shawara ga ‘yan’uwa da za su karanta littafin “Tuhfatul Maudud” na Ibnul Ƙayyim (Radiyallahu Anhu).

## SIFFOFIN MASU BA DA TARBIYYA

Masu hikima suna cewa: In mutum ya ce zai ba ka riga to ka dubi ta jikinsa kuma "wanda ba shi da abu ba zai iya bayar da shi ba.”

A kan haka ya wajaba a akan duk wani wanda nauyin tarbiyya ya hau kansa iyaye, malamai da shugabanni ya kasance mai tarbiyya ne shi akan kansa.

Wani mutum ya tambayi malamansa cewa ya koya masa yadda ake yin tarbiyyar ‘ya’ya a lokacin ‘yarsa ta fari tana wata ɗaya da haihuwa, sai malamin ya ce da shi ai kuwa ka makara. Saboda ita tarbiyya tun kafin a yi aure ake fara yinta ba sai an haifi ɗan ba.

Malamai sun yi bayanin siffotin da ya wajaba mai ba da tarbiyya ya siftantu da su in dai yana son ya sami nasarar aikin tarbiyya kuma ya yi tasiri.

## A TAƘAICE GA WAƊANNAN SIFFOFI:

1. Ya kasance mai haƙuri da juriya da naci, kada ya ɗauka cewa tarbiyya aiki ne na sha yanzu magani yanzu.
2. Ya yarda cewa haƙƙi ne wajibi a kansa. Ya rinƙa jin haka a ransa a kowane lokaci. wannan zai hana shi yin watsi da tarbiyyar iyalinsa.
3. Ya rinƙa sa ido da lura da bibiya, saboda tarbiyya kamar dashe ne in ba a bibiyarsa da kula da shi sai yå bushe ya lalace ko dabbobi da ƙwari su kashe shi.
4. Yi dan Allah (Ikhlasi) kada mutum ya nemi wani lada ko yabo a kan tarbiyyar 'ya yansa da iyalınsa sai a wurin Allah kawai. Saboda haka ban da alfahari ban da fariya ban da gorantawa ‘ya’ya da iyali ban da raina ‘ya’yan wasu.
5. Tarbiyya tana buƙatar tausasawa da bin al amura sannu-sannu daki- daki. tsanani da gallazawa kawai ba sa kawo gyara. dole sai ana cizawa ana hurawa.

Mai ba da tarbiyya shugaba ne, saboda haka ya kamata ya siffantu da siffofi na shugabanci ya kasance jarumi, mai adalci. mai kwarjini, mai iya ɗaukar nauyin waɗanda yake jagoranta, mai kyauta, sauƙin kai da saussauci a inda ya dace, mai tsanani a inda ya dace, da dai sauran siffofi na jagora ko shugaba na gari.

Harkar tarbiyya ba abu ne da ake yinsa da ka ba, lallai sai an yi karatun tarbiyyar saboda tana farowa, tun kafin a auri uwar da har ta haife shi ya balaga, za a yi masa tarbiyyar jiki, Imani, halaye, ladabai, haƙƙoƙi, siyasa da sha'awa. To in ba ilimi ta yaya wannan aiki zai yiwu

8 Wajibi ne mai tarbiyya ya kasance mai adalci. Ya kasance yana ɗaukar matakai na gasakiya a komai ya daidai ta tsakanin tsanani da sassauci da sakin hannu da rowa. ya kasance tsaka-tsaki a komai.

9 Wanda yake da tsananin rowa da kankamo da masifar son abin duniya ba zai iya tarbiyya ba. Dole ya kasance mai sakin hannu da sakin fuska. Kada ya ɗauka asarar kuɗi yake yi in ya biya kuɗin makaranta ko ya sai abinci da sauran buƙatun 'ya yansa.

10 Ya kasance mai nuna ƙauna ta gaskiya ga' ya'yansa maza da mata 'ya'yan uwar gida da na amarya.

11 Dole ne mai tarbiyya ya kasance nutsattse mai hankali da tsari a rayuwarsä.

12 Wajibi ne mai tarbiyya ya kasance ya siffantu da kyawawan halayen da yake umarni da a aikata su. Yana nisantar munanan ayyukan da yake hanawa. Kada ya zama fitina ga waɗanda suke a ƙarkashinsa.

13 Ya kasance mai kyakkyawan fata da sakakkiyar zuciya kada ya rinƙa camfa abubuwa ko saurin siƙewa da fidda rai kan samun nasara.

14 Ya kasance mai jin ƙai da tausayi.

15 Ya kasance mai tsoron Allah (Taƙawa) wannan sharuɗɗa muhimmancinsa ya gawurta.

KURA-KURAN MASU BA DA TARBIYYA

lyaye da malamai da sauran waɗanda nauyın tarbiyya yake kansu sukan tafka waɗansu kura-kurai da sukan kawo cikas ga tarbiyyar "ya ya ko ma gaba ɗaya a rasa tarbiyyar. Waɗannan kura-kuran suna da yawa, ga kaɗan daga cikinsu.

**1.Magana daban aiki daban**

Misali iyaye za su hana 'ya'ya zagi ko ƙarya ko saɓa alkawari ama su suna yi.

**2..Saɓani tsakanin masu tarbiyya**

Misali Uwa ta ce yi kaza Uba ya ce kada ka yi, ko ka ga a gida ana rusa abinda aka koyar a makaranta, ko akasin haka.

**3..Gallazawa da tsanantaw**

ani horon yakan zama azaba kamar hana yaro abinci, yi masa dukan kawo wuƙa, korarsa daga gida, ɗaure shi da sauransu, wannan ba ladabi ba ne.

**4.Rainon yaro a kan tsoro da ragwanci**

Tsanani da takurawa in suka yi yawa sai yaro ya taso da tsoro da gaulantaka.

**5.Shagwaɓa**

Bai kamata saboda tsananin ƙauna har kuma a bar ɗa ya zama shagwaɓaɓɓe ba, ba faɗa ba kwaɓa ba a ganin laifinsa har iyaye su rinƙa rigima da malamai da duk wanda ya yi ƙoƙarin tsawatar da ‘ya’ya kan wani abu maras kyau.

**6.Nuna bambanci**

Nuna bambanci a tsakanin ‘ya’ya yana da mumnmunan tasiri da kawo cikas ga tarbiyyar su da zumuncinsu da ma biyayyarsu ga iyayensu.

**7.Barin 'ya'ya a hannun 'yan aikin gida ko masu raino.**

Waɗansu iyayen saboda isa ko wayewa ko aiki sai su fice su bar ‘ya’yansu a hannun masu raino, ko su kai su gidan raino sai sun dawo su ɗauke su. Wannan babban kuskure ne.

**8.Raina 'ya’ya**

Yaro yana so a mutunta shi. amma a wajen waɗansu iyaye Ko da ya yi jikoki to yana nan dai a yaro bai isa komai ba. Wannan kuskure ne.

**9.Amfani da kayan Sadarwa:**

Cikakken ‘yancin amfani da kayan sadaarwa na zamani ba tare da wata kulawa ba. wannan ya ya matuƙar gurɓata tarbiyya

**10.Ƙwauro da rowa.**

Misali: Ƙin kashe kuɗi a bangaren ilimi, lafiya ci da sha da sutura alhali akwai ikon yi.

**11.Ƙin sa su aiki**

Komai sai a sa almajurai da ‘yan aikin gida, su yara ba abinda suka sani sai Su wanke goma su tsoma biyar

**12.WulaƘanta 'ya'ya da cin zarafin su.**

**13. Tsananin kyautata zato, da tsananin munana zato**

Wasu iyayen ba sa yarda da laifin 'ya'yansu, komai suka yi sai su ce shari a ka yi musu, in kuma a gabansu suka yi sai su ce ba halinsu ba ne ‘ya' yan wane ne suka koya musu. Waɗansu kuma kullum cikin tuhuma da zarginn 'ya'yan suke. Basa nuna jin daɗinsu da murna ga wani ƙwazo na ‘ya’ya sai dai kullum su rinƙa gwale su, su kashe su. Duka wannan kuskure ne.

**14. Baƙar addu'a**

Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya hana a yi wa 'ya'ya da iyali da dukiya baƙar addu'a. Saboda in Allah ya amsa sai su lalace.

**15. Kura-kurai lokacin haihuwa**

Sun haɗa da jin haushin abinda aka Haifa saboda mace ce ko namiji ne, sa masa suna marasa kyau, ƙin yin haƙiƙa (ragon suna) alhali akwai ikon yi, jinkirin yin kaciya. ƙin sayan kayan jarirai, gallazawa da baƙantawa mai jego da sauransu. Ya kamata masu ba da tarbiyya su guji waɗannan kurakuran da ire-irensu. Allah ya tainmake mu.

MATAKAN TARBIYYA GUDA 100

A wannan matashiya zan kawo taƙaitattun bayanai kan mataki da hanyoyn tarbiyya da ya Kamata iyaye su yi ta mamaita karanta waɗannan bayanai su kuma haɗa kai wajen aiwatar da su domin samun zuri a managarciya mai amfani ga kowa, zuri'a da za ta samu lada mai ci gaba bayan mutuwar iyaye. Allah ka sa mu dace.Amin

**1.Tausayi da jin ƙai**

Ya kamata iyaye su kasance masu tausayi da Jin ƙai da bi sannu-sannu wajen tarbiyyar ‘ya’ya. Su yi koyi da Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) yadda yake tausayawa ƙananan yara yake jan su a jiki.

**2.A guji zagi tsinuwa**

Waɗansu iyayen sukan ɗauka gallazawa da tasnantawa da zagi da la'anta da ɗaure fuska shi ne kaɗai zai sa ɗa ya taso da tarbiyya. A gaskiya wannan kuskure ne babba.

**3.A guji azabtarwa da yawan duka**

Wannan ma kuskure ne ta yadda za ka ga waɗansu iyaye har hana ‘ya’yansu abinci suke yi, ko su yi musu zigidir su zane su, wannan yana da mummunan tasiri a fannin tarbiyya.

**4.Koyarwa**

Ya wajaba a rinƙa koyawa 'ya'ya abinda zai amfane su da abinda zai cutar da su. A yi wannan koyarwar mataki-mataki gwargwadon shekaru da fahimtar yaro.

**5.**Wasiyyar lukman (Alaihis Salam)

Ya kamata a ɗora tarbiyyar ya'ya kan wasiyyar Lukman (Alaihis Salam) ga ɗansa wacce Allah Ta ala ya kawo ta a suratu Lukman aya ta 12-19. Domin ta ƙunshi gaba ɗayan turakun tarbiyya. Yiƙoƙari ku karanta waɗannan ayoyi tare da sanin ma anoninsu.

**6.Koyar da ladabi**

Ladabi shi ne gishirin zaman duniya, wanda ba shi da ladabi komai iliminsa komai kuɗinsa komai mulkinsa ya yi asara. Lallai ne a koya wa ‘ya’ya ladabin zama da kowane irin rukuni na mutane, ladabi ga Allah da Manzonsa da Alƙur’ani da sauransu.

**7.Tsoron Allah Ta'ala**

A cusawa yaro aƙidar tsoron Allah Ta' ala da yarda da cewa duk inda mutum yake Allah yana jin sa yana ganinsa yana sane da duk abinda yake aikatawa, babu abinda yake ɓuya a gare shi.

**8. Imani da Alƙiyama**

A dasa masa wannan a zuciyarsa, ya yarda cewa a wannan rana. Allah zai yi sakamako ga kowa kan abinda ya aikata na alheri da aljanna ko na sharri da wuta.

**9.Ladabi ga Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam)**

A koyawa 'ya'ya ladabi ga Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ta yadda za su yi cikakken imani da shi, su rinƙa girmama shi, kada su yi masa kishiyoyi, su sallama masa, su ƙan ƙame sunnarsa su tsani bidi 'a, su guji munana ladabi a gare shi.

**10.Ƙaunarsa da sahabbansa da iyalansa**

A dasa ƙaunar Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) da sahabbansa da iyalansa (Radiyallahu Anhum) a zukatan 'ya ya ta yadda za su rinƙa koyi da su. Su guji aƙidar ƙin sahabbai da zaginsu da allanta iyalan Annabi (Sallallahu Alaihi Wasallam)

**11.Ladabi ga Al-ƙur'ani**

Su yi imani da shi, su rinƙa ƙaunarsu., su haddace shi su san ma'anarsa, su rinƙa aiki da shi a kowanne ɓangare na rayuwarsu. Su ringa girmama shi ya zama shi ne jagoransu a rayuwa.

**12. Bin Iyaye**

Lallai a koya musu biyayya ga iyayensu, musamman Uwa.Su ringa girmama su, su rinƙa yi musu godiya, da tausaya musu da taimakonsu da kaucewa saɓa musu. Yana daga ladabi ga iyaye sakaya sunayensu, Kada ɗa ya Jawo musu zagi, kada ya ɗaga muryarsa sama da ta su ya yi Magana dasu cikin tausasawa da ganin girma.

**14. Babu biyayya Cikin saɓon Allah.**

A sanar da 'ya'ya cewa babu wani mahaluƙi kowane ne shi da za a yi masa biyayya in ya yi umarni da saɓon Allah Ta'ala ko Manzonsa (Sallallahu Alaihi Wasallam).

**15.A kyautata musu koda sun kauce hanya**

ƙin bin iyaye akan saɓawa Allah Ta'ala ba ya nufin a daina kyautata musu, a'a aci gaba da kyautata musu ammakada a yi musu biyayya a kan saɓon Allah Ta ala. A koyar da 'ya ya wannan.

**16. Koyi da Annabawa da Salihan bayi.**

A nunawa 'ya' ya cewa a faɗin duniyar nan babu waɗanda suka cancanci a yi koyi da su sai Annabwa da Sahabbansu da sauran bayin Allah nagari. Su guji kwaikwayon maƙiya Allah maƙiya addinin Allah da Manzonsa.

**17.Girmama Malamai**

A koya musu girmama malamai da martaba su, kada su rinƙa kiransu da sunayensu ballantana da sunan banza.Kada a rinƙa kushe malami a gabansu, a nuna musu cewa malami uba ne.

**18.Umarni da Salla**

A tilasa su su rinƙa yin Salla daga shekara bakwai in sun shekara goma suka ƙi yin salla a doke su. Kafin su shekara bakwai a rinƙa lallaɓa su da kwaɗaitar da su a kan salla.

**19. Alamomin Balaga**

Tun kafin su balaga ya wajaba iyaye da malamai su sanar da su alanomin balaga da sanar da su cewa da zarar sun ga waɗannan alamomi to fa dokokin Allah sun hau kansu,kada su yi ta ɓarna ko su yi ta wasa da ihu dan suna jin cewa wai su yara ne.

**20.Umarni da kyakkyawa da hana mummunan aiki.**

A sanar da ya' ya kyawawan ayyuka da kishiyoyinsu a koya musu hanyoyi umarni da kyawawan ayyuka a hana munana bisa koyarwa Ƙur'ani da sunna da bin salon magabata na Ƙwarai

**21.Girmama manya da tausayawa Ƙanana**

iyaye su koyawa ya' yansu su rinƙa yi wa duk wanda ya girme su kallon Uba ko Uwa, na ƙasa da su kuma su ɗauke su a matsayin Kannai. Su girmama manya su tausayawa ƙanana su yi kyakkyawar mu'amala da sa'o insa a matsayin abokai.

**22.Kula da kyawawan halaye**

lyaye su ɗora 'ya yansu a kan halaye na haƙuri, juriya, wadatar zuci, nutsuwa, da mutunci Su nisanta da munanan halaye kaimar girman kai, alfahari. wulaƙanci da sauransu.

**23. Wasiyyar Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ga Ibn Abbas**

Lallai ne iyaye su tarbiyanci 'ya yansu akan Waɗannan abubuwa su ne: Bin dokkin Allah a kowanne hali. roƙon Allah da neman taimakonsa shi kaɗai, dogaro gare shi da rataya zuciya gare shi shi kaɗai, sai ƙarfin hali da jajircewa da kyakkyawan fata a rayuwa. Wannan hadisi shi ne hadisi na 26,669 a Musnad na Imam Ahmad na 2516 a Timizi na 19 a Arba' una Hadis.

**24. Wasiyyar ƙarfafa gwiwa**

Haka nan ya kamata a ɗora yara a kan wannan wasiyyar ta Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) wacce yake cewa: "Mumini mai ƙarfi ya fi alhairi kuma Allah ya fi son sa fiye da mumini mara karfi. Amma kowanne yana da alhairi. Ka dage kan abinda zai amfane ka, ka nemi taimakon Allah. Kada ka gaza, idan wani abu ya same ka kada ka ce da na yi kazamda kaza ne zai faru. Kawai ka ce haka Allah ya ƙaddara kuma abinda ya ƙaddara shi ne yake kasancewa, saboda irin waɗannan maganganu suna buɗe kofar shaiɗan.

**25.Su guji kaɗe-kaɗe da wake-waƙe**

A yi wa 'ya 'ya tarbiyyar nisantar kaɗe-kaɗe da waƙe-waƙe saboda suna kashe zukatu suna koya ɓarna suna buɗe Kofofin sha'wa da fitintinu iri-iri.

**26. Nisantar hotuna da gumaka**

Asalin bautar gumaka ta faru ne daga kakkafa da liƙa hotunan bayın Allah daga nan sai aka sassaƙa gumakansu,sai aka kama bauta musu. A yanzu abin jiya ya fara dawowa saboda haka a yi hattara. Hoto in dai ba na lalura ba ne kada a yi sai dai hotunan abubuwa marasarai ko waɗanda za a rinƙa tattaka su ana wulaƙanta su amma ba girmamawa ba.

**27. Nisantar kafirci da danginsa**

A dora 'ya ya a kan nisantar da ƙyamar kafirci da danginsa wato aiki na shirka da saɓo irinsu zage-zage shaye-shaye.maganganun batsa, caca, karance-karancen batsa da soyayya, tsafi da camfe-camte da sauransu.

**28.Yabawa yaro in ya yi abin kirki.**

Yana daga hanyoyin tarbiyya a yabawa yaro in ya yı abin kirki a yi masa addu'a, amma kuma kada a yi masa yabon da zai sa masa girman kai ko kuma duk lokacin da ya yi kirki ya saurari yabo, ta yadda kuma zai koma yin abu ba don Allah ba, sai don a yaba masa.

**29.Salla da addu'ar Istihara**

Tun da wurwuri a koyawa yara yadda ake yin istihara don su kaucewa istihara ta bidi'a da bokanci. Saboda Manzon

Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) yana koyar da istihara kamar yadda yake koyar da Karatun Ƙur'ani.

**30.Ba da kyauta**

Ba da kyauta ko wata shaida ta yabo kan kula da salla ko ƙoƙari a makaranta da sauransu abu ne mai kyau a fannin tarbiyya. ldan wani ya yi ƙoƙari an ba shi kyauta to shi kuma wanda bai yi ƙoƙarin ba sai a dubi wani ɓangaren da ya yi koƙari a kansa kamar tsafta ko kula da salla a yi masa kyauta a Kan wannan.

**31.Yin faɗa da nasiha a ɓoye**

Idan yaro ya yi laifi kada a yi masa faɗa ko nasiha a gaban yan uwansa, a'a ya kamata ayi masa a keɓance musamman in abinda ya yi ba halinsa ba nc, ko kuma ya yi ne a ɓoye.

**32.Ya san dalilin horo**

Hanyoyin horo suna da yawa sun haɗa da: daure fuska. ƙin yi masa Magana, hana shi abin wasa, ko yin wasan, ba shi hadda ko wani rubutu da sauransu, ba duka ne kawai hanyar horo ba Kuma ya san dalilin da ya sa aka yi masa horon.

**34.Horo da duka**

Ba a yin horo da duka sai bayan an yi gargaɗi an bi dukkannin hanyoyin da suka gabata ba su yi amfani ba.Kuma ya san dalilin dukan, kada kuma a yi duka a fuska da maƙarfafa, kada a haɗa da zagi ko wani abu na wulaƙanci,kuma dukan ya kasance sama-sama.

**35.Adadin bulala**

Ba a dukan yaro a kan barin haƙƙin Allah Ta'ala sai ya kai shekara goma kuma ba a wuce bulala goma tare da sharaɗan da suka gabata.

**36. Ku kasance abin koyi ga 'ya'yanku**

Mai dokar barci bai kamata ya yi gyangyaɗi ba. Saboda haka ya wajaba iyaye da malamai da dukakkanin manya su kasance managarta domin yara da su Suke koyi. Kada a rinƙa faɗa ba aiki, ko aiki ya rinƙa saɓawa magana.

**37. Haɗin Kai**

Ya kamata Uwa da Uba bakinsu ya zo ɗaya a kan tarbiyya kada su raba hankalin ɗa wannan ya ce yi, wannan ta ce kada ka yi, wannan yana da hatsari babba.

**38. Lallai ne Uwa da Uba su ɓoye duk wani saɓani da**

yake a tsakaninsu ta yadda ‘ya’yansu ba za su fahimci me ake yi ba. Kada su yi ko da musu a gabansu ballantana dambe da zage-zage

**39. Sai fa an haɗa da naci**

Tarbiyya a wannan zamanı tana bukatar naci da haƙuri da yawan maimaitawa ɗa bibiya, saboda yawaitar masu rusa tarbiyya da matsanancin naci da maimaita ɓarna da suke yi ba dare ba rana da hanyoyi da salo daban-daban.

**40. Yanayi mai kyau**

Ya kamata a samar da yanayi mai kyau na tarbiyya wannan yanayi ya haɗa da auren mace/miji managarci/managarciya da samun maƙota da abokai da malamai managarta. In waɗannan suka haɗu tabbas za a samu tarbiyya in sha Allah.

**41. Abokai da malamai nagari**

Ya kamata iyaye su taimakawa ya yansu wajen zaɓa musu abokai da ƙawaye da malamai nagari. Saboda zama tare yana da tasiri ƙwarai da gaske wurin kwaikwayo da nason hali.

**42. A raba su da muggan abokai da ƙawaye**

Ya wajaba su hana 'ya'yansu yin abota da lalatattun abokai da ƙawaye cikin hikima da dabara ba tare da nuna musu cewa su tsarkakakku ba ne. waɗancan kuma wasu najasa ne.

**43. Kada ku yi nesa da ya'yanku**

Ya kamata duk inda ya' ya za su je ya kasance da sanin iyayensu, iyaye mata su rinƙa zama da ‘ya’ya mata su kuma ya su rinƙa tafiya da 'ya'ya maza wurin ayyukan alhairi, Saboda su saba kuma su rinƙa koya musu kyawawan halayensu.

**44. Siffofin malamai**

A nutsu sosai wurin zaɓar malaman da za su koyar da ‘ya'yan su kasance masu mutunci da hankali da ladabi da ilhami, da riƙo da addini da hikima da tsafta da tausasawa.

**45. Malamai su haɗa kansu**

Malamai a matsayinsu na ginshiƙi a fagen tarbiyya ya kamata Su haɗa Kansu kada wani yana tufka wani yana warwarewa. Kada malamin wani fannin ya raina na wani fannin.

**46. Son ya zo na ɗaya a kowane fanni**

Ya kamata malamai da iyaye su dasawa ya'ya son da ƙaunar da gasa da juna wajen zama na ɗaya a kowane fanni na rayuwa. Kada su taso da aƙidar "da ƙyar na sha ya fida ƙyar aka kama ni a’a kada ma a ce an biyo ka da gudun tuni ka yi gaba shi ya fi.

**47. Karatu a gida**

Lallai ne duk runtsi da kujiba-kujiba a ware lokaci a gida da za a rinƙa karatu na gaba ɗaya a maida hankali wajen karatun hadisin kwaɗaitarwa da tsoratarwa da fiƙhu da tafsiri da sira da arabiyya.

**48. Ɗabi'ar Karatu**

Ya kamata iyaye su koyawa 'ya'yansu ɗabi'ar yawan karance-karance da son karatu da tara littattafai, kada a bar Su su yi wa komfuta matsanancin sabon da za ta sa su Ƙauracewa karatu da littafi.

**49. A samar da laburare**

Samar da daƙin karatu in da hali a gida, ko yin wasu ‘yan kantoci da jera littattafai a cikinsu da ake karantawa, zai taimaka wajen cusawa 'ya' ya ɗabi'ar son karance-karance.

**50. Kwana a gida ‘yan uwa**

Ba da dama ga ‘ya’ya su rinKa ziyartar gidanjen dangi ka kai su har ma su kwana in ta kama, wannan abu ne da yake koyawa 'ya ya zama da mutane da mu amala da su da sabo da rashin abinda aka saba da shi

**51. Shiga Cikin Jama'a**

Kada a ƙuntatawa yaro a cukwikwiye shi a gida ba ya zuwa ko'ina ba ya hulɗa da kowa daga makaranta sai gida, a rinƙa ba shi damar shiga Cikin jama a da halartar sabgogi da suka dace da shari'a da shekarunsa, a bisa kulawa da sa idon iyaye da yan uwa.

**52. Yin raha da yara**

Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya kasance mai sakin fuska yakan yi raha da kakaci har da ƙananan yara. Saboda haka lokaci zuwa lokaci iyaye su rinƙa yin raha da 'yan wasanni da ya yansu waɗanda suka dace da sheckarun kowannensu.

**53. A Koya musu siye da siyarwa**

Ya kamata iyaye su koyawa 'ya yansu wayewar saye da sayarwa gwargwadon shekarunsu. Kada a bari har su girma ko ƙirga ba su iya ba, ko ma ba sa iya bambamcewa tsakanin takardun kudi ballantana saye da sayarwa.

**54. Riƙe sirrin gida.**

A koyawa 'ya' ya riƙe sirrin gidansu da sauran abubuwan da suka shafi iyali, kada a bari yawan surutunsu ya kai matsayin da har zai je waje yana yaɗa sirrin gidansu.

**55. Kada ya rinƙa faɗar matsalolinsa**

A sanar da ya'ya cewa bai kamata su rinƙa fadar matsalolin da suke ciki ba, sai ga wanda yake ganin zai iya ba shi mafitar warware wannan matsalar kamar iyaye da malamai.

**56. Daidaita kishi da gasa**

Dukkan ɗan Adam yana da ɗabi'ar ƙananan yara, wannan ne ya sa wa yake kishi da ƙanınsa Jariri shi ma yana son a rinƙa ɗaukarsa da sauran kulawa kamar a da, to anan iyaye su saita wanan ɗabi'a Cikin hikima kamar a ɗauke hankalinsa da wani abin wasa. A juyar da ɗabi ar gasa wurin karatu da sauran ayyukan alkhairi

**57. Addu'a**

Kada iyaye su gaza ko su ƙosa wajen yiwa 'ya' ya addu'ar neman shiriya da nagarta A rinƙa bibiyar lokutan anmsa addu'a a rinƙa yawaita sadaka da kyautatawa malamai da mabuƙata a kan wannan manufa

**58. Banda baƙar Addu'a**

Duk bacin ran da iyaye za su shiga su iya bakinsu kada su kuskura su yi wa 'ya' yansu baƙar addu'a ko baki. Wannan abu ne mai hatsarin gaske a kan dukkan al'umma.

**59. Bayar da tsaro**

Ya wajaba iyaye su kula sosai da tsaron lafiya da hankali da. mutumcin ‘ya’yansu. Su daina sakinsu kamar dabbobi musamman farkon dare lokacin da shaiɗanu suke fara dabdalarsu.

**60. Hana kwanciyar rub da ciki**

Manzon Allah (Sallallahu Alaihi Wasallam) ya ga wani ya kwanta rub da ciki sai yace: "wannan kwanciyar Allah ba ya son ta (Abu Dawud,Timuizi, Ahmad). Kuma likitoci sun tabbatar da cewa wannan kwanciyar cike take da illoli da jawo cututtuka.

**61. Nisantar da motsa sha'awa**

A kula da abubuwa masu motsa sha awa a rinƙa nesanta yara daga gare su, kamar kwanciyarsu a mayafi guda,cuɗanyar maza da mata, bayyana tsiraici kalle-kalle da karance karance soyayya da batsa.

**62. Kau da kai daga kallon tsiraici**

A tarbiyyar yara a kan runtse idanu kan kallon mata da tsiraici ta hanayar karantawa da nisantar na' urori masu yaɗa hotuna da fina-finan batsa.

**63. Koya wa mata suratun Nur**

Suratun Nur ta ƙunshi hukunce-hukuncen hijabi da neman izini da sauransu, saboda haka Sayyadina Umar yake ba da umarni ga wakilansa su rinƙa koyawa mata wannan sura tare da bayanin ma anoninta.

**4.Su nisanci lalata.**

Tun da wuri a sanar da yara haramcin zina luwaɗi da Maɗigo ta hanyar da ta dace da fahimtarsu da shekarunsu.

**65. Kare mutunci da matsayi**

A cusawa yara kishin kare mutuncinsu da matsayinsu. A koya musu cewa duk abinda ba ka so a yi maka to kada ka yi wa wani. ka tsare mutuncin mutane sai a tsare maka naka

**66. Kunya**

Kunya tana daga Cikin imani, a koyawa yara ɗabi’ar jin kunya bayyana tsiraici da sanya matsattsun kaya masu bayyana tsiraici da jin kunyar saɓawa Allah da shiga haƙƙin mutane.

**67. Daga shekara Bakwai**

Tarbiyyar suturce jiki da sanya cikakken hijabi ga mata ya kamata ya fara tun daga shekara bakwai na rayuwar 'ya ya.

**68. Idan mace ta balaga**

A yayin da yarinya ta balaga ta hanyar fara al'ada ya wajaba ta rinƙa rufe gaba ɗayan jikinta kafin ta fita, ko a lokacin da take tare da wanda ba muharraminta ba.

**69. Kowa ya sanya kaya irin nasa**

Lallai ne iyaye su kula da suturun ya yansu, maza su sa kayan maza, mata su sa kayan mata.

**70. Ban da kwaikwayon kafirai da fajirai**

Kada iyaye su ƙyale 'ya'yansu suna kwaikwayon suttura da ɗabi'u na kafirai da watsattsun mutane irin waɗanda ake ganinsu a kafafen sadarwa da sauransu.

**71. Auren Wuri**

Ya kamata iyaye su tamakawa 'ya'yansu maza su yi aure da wuri muddin sun samu sana'a da nutsuwa da ilimi daidai gwargwado, Kada a ƙyale su har su ƙosa ba aure, saboda babu abinda zai magance yawaitar lalata sai aure.

**72. Daƙile aƙidar tsarin iyali**

Tsarin iyali wani abu ne da yanzu yake nema ya zama kamar wani abin yayi. Wannan tsarin yana da illoli masu yawa na kusa da na nesa. A koyar da matasa masu aure da masu shirin yin aure illolin tsarin iyali. A koyar da su hanyoyin faɗaɗa sana'o'i a inganta su da Kuma tarbiyyar wadatar zuci.

**73. Tarbiyyar sha'awa**

Addinin musulunci ya koya yadda ɗan Adam zai sarrafa sha'awarsa ya bayyana halal da haram da hanyoyin riga kafin aikata laifuffukan jinsi, ya wajaba ‘ya’ya su san wannan tsarin da hukunce-hukuncen tun kalin balagarsu.

**74. A rinƙa yin kinaya**

Dukkan baiyanar da koyarwa da suka shafi alaƙar mace da namiji da maganar Jinsi ya wajaba su kasance cikin tsafta da amfani da kalmomi masu tsafta ban da gatsal-gatsal don gudun gyaran gangar auzunawa.

**75. Neman lzini**

A koya wa ‘ya’ya hukunce-hukuncen neman izini da sallama kafin shiga gida ko ɗaki wannan abu ne mai matuƙar muhimmanci da amfani.

**76. Hulɗa da mutane**

Ya kamata a koyar da 'ya'ya yadda ake hulɗa da kowane jinsi na mutane misali malamai iyaye, maƙota, shugabanni, 'yan Uwa, tsofaffi, masu buƙata ta musamman da sauransu.

**77. Shawara da su**

Yin shawara da 'ya'ya musamman a kan abinda ya shafe su da kuma harkar gida a lokacin da ya dace abu ne mai kyau kwarai da gaske a fannin tarbiyya.

**78. Tashen balaga**

Wannan lokaci ne mai muhimmanci da rikice-rikicce a rayuwar 'ya'ya. Yana farawa daga shekaru goma sha uku zuwa shekaru goma sha takwas. Ya wajaba iyaye su fahimci haƙiƙanin yadda wannan mataki yake da buƙatun yara a wannan lokaci da yadda ya kamata a ɓullowa matsalolin lokaci.

**79. Hira da 'ya'ya**

Ya wajaba iyaye su rinƙa zama suna yin hira da 'ya'yansu,a irin waɗanan lokuta ne, za su rinƙa koya musu ladaban hira da tattaunawa, da ma ilimin zaman duniya.

**80. Yawan Tambayoyi**

Kada iyaye su nuna ƙosawa ga yawan tambayoyi na'ya'yansu, kada su rinƙa kwaɓarsu a kan irin waɗannan tambayoyin. A ba su amsa gwargwadon hankalınsu. In tambayar ta fi ƙarfinka sai ka waske ta hanayar dabara.

**81. Saurararon 'ya'ya**

ldan yaro ya zo maka da matsala ko ya kawo maka ƙara ka tsaya ka saurare shi komai rashin muhimmancın matsalar shi a wajensa muhimmiya ce. da haka zai saba har ya rinƙa kawo. maka muhimman matsalolin. kuma ya koyi ɗabi'ar sauraron mutane da taimakonsu.

**82. Girmama yara**

Kada a rinƙa walaƙanta yara da nuna musu su kamar su ba mutanc ba ne. wasu iyayen har ɗa ya yi furfura yana nan a matsayin yaro a wurinsu. Wannan babban kuskure ne.

**83. Adalci**

Ya wajaba iyaye su yi adalci tsakanin 'ya'yansu maza da mata manya da ƙanana. 'ya'yan uwargida da 'ya'yan amarya. Wannan yana taimakawa sosai a fannin tarbiyya.

**84. Ciyarwa Ibada ce**

Ya kamata iyaye su sani cewa ciyar da iyali da kula da ɗawainiyarsu ta lafiyarsu iliminsu da sauransu 1bada ce.saboda haka su saki ransu su yi farin ciki ban da yi wa ‘ya'ya gori ko gaya musu maganganu da suke nuna ƙosawa ko jin hausnin ɗawaaniyar da yake yi.

**85. Banda shagwaɓawa**

Kada iyaye su shagwaɓa ‘ya’yansu a ƙarshe sai su zo su fi ƙarfinsu su gagari kowa.

**86. Kwanciyar hankali**

Duk wani abinda zai firgita yaro ya tayar masa da hankali ya kanmata a nisanta razana yana da mummunan tasiri a kan tarbiyyar 'ya' ya.

**87. Tarbiyar ya' yan fari**

Lallai iyaye su kula sosai da tarbiyyar 'ya yansu na fari.Kada doki da soyayya ta sa a bar su su sangarce. ldan na farkon suka gyara to haka ‘yan gidan za su taso, in kuwa suka karkace to haka abin zai ta tafiya. Wannan kuma ba ya nufin daga kun manyanta a dakata ba, a a, a ci gaba harkan ɗan auta.

**88. Tarbiyyar 'ya'ya mata**

A kula sosai da tarbiyyar 'ya'ya mata, saboda su ne masu raino da kula da 'ya'ya fiye da iyaye maza. in mata suka Samu tarbiyya duk al’umma za ta gyaru.

**89. A kula da marayu**

Lallai ne al'umma su kula da marayu a ba su ingantacciyar tarbiyya saboda maraici zai iya samun ya' yan kowa kuma ba a san irin amfanin da marayun nan za su yi ba ga al 'umma in sun sami tarbiyya mai kyau.

**90. Kalmar farko**

A yi ƙoƙari kalmar farko da yaro zai buɗi baki da ita ta kansance Laa ilaha illallahu.

**91. Girmama baƙi**

A koya wa ‘ya’ya girmama baƙi da yi musu hidima. Kada kuma su zauna su zura idanu su buɗe kunnuwa suna jin hirar da ake yi.

**92. Haƙƙoƙin hanya**

Hanya tana da haƙƙoƙin waɗanda suka haɗa da tafiya Cikin nutsuwa, da bin dokokin tuƙi tsaf tace hanya, kada a ci wani abu a wurgar da leda ko ɓawo a kan hanya. a kawar da abu mai cutarwa, kada a yi fitsarı ko kashi a kan hanya da sauransu. A koyawa yaro waɗannan ladabai.

**93. Lokacin Hutu**

A yi amfani da lokutan hutun ‘ya’ya wajen shirya musu abubuwa masu amfanı kamar tafiye-tafiye da wasanni masu ma’ana da koyon sana’o’i da karatuttuka na musamman.

**94. Wakilci**

Idan yaro ya ɗan data a rinƙa wakilta shi a kan waɗansu abubuwa da suka dace dan ya taso da tarbiyyar hulɗa da mutane.

**95. Cika alƙawari da gaskiya**

Kada ka yi wa ɗanka alƙawarin da ka san ba za ka iya ba. Duk abinda za ka faɗawa 'ya'yanka ka tabbatar gaskiya ne. kada ka rinƙa shara ta, sai gimanka ya faɗi kuma su ma su zama maƙaryata.

**96. Rarraba ayyuka**

Ka rabawa 'ya'yanka ayyuka kowa ka dubi abinda ya fi dacewa da shi saboda gida kamar masarauta ce, akwai buƙatar sarki, waziri, fadawa (masu ba da tsaro) da sauransu.

**97. Neman afuwa**

Ku koyawa 'ya'yanku ɗabi'ar yarda da amsa kuskure in Sun yi da kuma neman afuwa. Su ga misali daga gare ku.

**98. Fasaha**

A lokacin da yaro ya yi wani kuskure na magana ko ya yi shirme ka gyara masa don ya taso da hikima da fasaha.

**90. Kowa da irin baiwarsa**

Ya kamata iyaye su kula da bambance- bambancen da suke a tsakanin ‘ya’yanstu da irin baiwar da Allah ya yi wa kowane ɗaya daga cikinsu. Sai a sarrafa wannan baiwar da Allah ya yi wa Kowane ɗaya daga cikinsu ta yadda za amfani kansa da al’umarsa.

**100. Tsoron Allah**

Babban al amari mafi muhmanci a komai shi ne tsoron Allah a fili da ɓoye da neman ilimi da aiki da shi Ya Allah ka ba mu zuri'a managarciya.

KATAFILUN RUSHE TARBIYYA

Dukkanin waɗannan matakai na tarbiyya da aka bayyana ba za su yi amtani a ga tasirinsu a ƙasa na samar da ingantacciyar al’umma ba, tilas sai an aiwatar da su. Sai kowa ya ɗauki aikin da yake kansa ya yi shi da gaske kuma saboda Allah Ta'ala. Sai dai kuma, a wannan zamani namu mutane masu yunƙurin gina tarbiyya sun yi ƙaranci ƙwarai da gaske, ga kuma ƙarancin kayan aiki da suke fuskanta wato ilimi da siffofin nan na masu tarbiyya da aka ambata. Yayin da ɗaruruwan dubunnan mutane waɗanda ba su da wani aiki sai ruguza duk wani gini na tarbiyya, wani ginin ma ana cikin yi suke zuwa su tarwatsa maginan su rushe shi, kuma suna da ɗimbin magoya baya cikinsu har da waɗansu masu ginin tarbiyyar! Amma duk da haka in aka yi wa gini kyakkyawa kuma kaƙƙarfan harsashi to babu yadda zaayi su iya taɓa wannan ginin ballantana su rushe shi.saboda haka kada magina tarbiyya su razana ko gabansu yafaɗi ko su karaya su dage su yi ta aiki ba dare ba rana Allah yana tare da su ba zai taɓar da aikinsu ba.

Abinda nake nufi a nan shi ne, abubuwan da suke rusa tarbiyya ko su hana ta tasiri a wannan zamani suna da matuƙar yawa kuma suna da ƙarfi da goyon baya sosai, amma duk da haka in mutum ya isaya ya jajirce sai Allah Ta'ala ya kare shi daga sharrin waɗannn maɓarnatan. A garguje zan faɗi kaɗan kuma manya-manya daga Cikin Waɗannan abubuwan da suke lalata da gurɓata da ma rusa tarbiyya domin duk wani mara son ya ga ‘ya’yansa da matansa da ɗalibansa da ma shi kansa. su sami ingantacciyar tarbiyya ta Musulunci Su faɗaka su ɗauki matakin gaggawa su kartata ginmsu tun kafin gabatowar rusau. Ya Allah ka tsare mu mu da zuri’armu.

**1.Yaɗuwar lalata**

Yaɗuwar lalata da shegantaka iri-iri a ko ina su ne manyan katfilu da suka fi saurin ruguguza tarbiyya. Zinace-zinace, Luwaɗi, Maɗigo, auren hannu sun yi matuƙar yawa kuma sun kafu sun sami goyon baya a Cikin al 'umma.

Hanyoyin yaɗa su da sauƙaƙa aikata su kullun sai ƙaruwa suke yi. Duk inda mutum ya duba hagu da dama gaba ɗa baya gida da waje sai ya ga tsiraici, ko dai ka ga mata ba hijabi ko ka gan su ana talla da su tsairara a jikin kwali ko gwangwani kusan duk wani kayan kantı. Su kuwa kafafen yaɗa labarai da hanyoyin sadarwa na zamani aika-aikar da suke yi ta ruguza tarbiyya abin sai dai addu'a,

A ɓangaren hukumomi kuwa, ai ko a jikinsu sai dai ɗan abinda ba a rasa ba.Saboda haka, ya wajaba kowa ya yi iya yinsa wajen yakar Waɗannan munanan ɗabi'u ta hanyar bin ƙaidojin tarbiyyar sha’awa da bayaninsu ya gabata a : Maƙalar mai taken: zuwa abokai na ango da maigida.

**2.Sakin Aure**

Duk da cewa an halatta yin saki a Musulunci, to amma Allah ba ya son sa, shi ya sa aka sanya tsauraran sharaɗai

da hanyoyın riga-kafi kafin a yi sakin, in kuma an yi akwai waɗansu dokokin da suke biyo bayansa. Yawan sakin aure barkatai ba tare da la'akari da makomar 'ya'ya ba. yana jefa tarbiyyarsu cikin wani mummunan hali wanda in ba a yi sa a ba daga nan sai dai shaiɗan ya cafë su ya ci gaba da yi musu irin ta sa baƙar tarbiyyar ta shaiɗanci. Saboda haka, wajibi ne miji da mata su guji yi wa juna abinda zai jawo rabuwar aurensu, in kuma ya zama dole sai an rabu to tadbatar an samawa tarbiyyar 'ya'ya kyakkywar makoma.

**3. Lalatattun abokai da ƙawaye**

A lokacin da yaro ko yarinya suka shekara 13 zuwa sama.za su rinƙa jin su fa yanzu sun girma, saboda haka sai alaƙarsu da mutan gida ta fara raguwa, sai ta ƙullu sosai da abokai da ƙawaye, wannan lokaci ne mai matuƙar hatsari a rayuwar ɗan Adam, a cikinsa ake gina mutum ko a rusashi. Mafi yawancin waɗanda suka lalace sun koyı lalatar ne daga abokai ko ƙawaye. Saboda haka ya wajaba a kan iyaye da malamai su sanya ido sosai a kan abokai da ƙawayen 'ya'ya da ɗalibai. a raba su da lalatattun a haɗa su da managarta.

**4.Shaye-shaye**

A halin yanzu. shaye-shaye ya zama wata musiba ba ga samari kawai ba har ma da "yan mata da matan aure. Wannan bala'i yana hana duk wani mai hankalı da fatan alhairi ga wannan al 'umma yın barci da idanu biyu a nute. Illolin shaye-shaye kuwa ga tarbiyya wannan ba sai an faɗa ba. Ya zama wajibi a kan kowa ya tashi haiƙan wajen yaƙar wannan mumunnar ɗabi a tun kafin gaba ɗayan al'ummar nan ta mu ta rikiɗe ta zama 'yar ƙwaya Alah ya kiyaye, saboda abin ya zama annoba ya zama wutar daji.

**5.Rashin abin yi**

Zaman yara musamman matasa ba aikin fari bare na baƙi sai dai kawai su ci su sha su sa kaya su fita yawo su dawo su sake ci su yi barci, wannan hatsari ne babba ga tarbiyya.Ya zama dole ga iyaye su rage son hutu ga 'ya'yansu su rinƙa shagaltar da su a lokutan da ba sa komai da aikace-aikacen gida, ko koyan sana'a ko kasuwa ko dai wani abun alhairi da zai cike gurbin zaman kawai da suke yi, in kuwa ba haka ba. to fa shaiɗan yana da ayyuka iri-iri masu ɗaukar hankali wadanda yake sanya masu zaman banza su yi masa kyauta.

**6. Hanyoyin sadarwa na zamani**

Wannan ma a yanzu ba ya buƙatar sharhi, kowa ya san irin mummunar illar da waɗannan katafe na yanar gizo na fesbuk da sauransu suke da shi wajen rusa tarbiyya da yaɗa ɓarna a iri-iri kamar zina, luwaɗi, maɗigo sata., kashe-kashe. shaye-shaye kai har ma da kafirci.Saboda haka, iyaye "nafsi-nafsi ku ceto kawunanku da 'ya'yanku da matanku daga halaka.

Ku nisanci waɗannan matsaloli sai ta hanya mai amfani. A guji fina-finan Hausa da na Indiya da na cana da na Turanci. Inkunne ya ji ************

**7. Sakacin Iyaye**

Sakacin iyaye da tsananin shagwaɓa ‘ya' ya, ko kuma kawai a haife su a yadda su wani ya tsinta, wato a yi watsi da tarbiyyarsu da haƙƙoƙinsu da Allah ya wajabtawa iyaye shi ma babbar katafila ce da take ruguje tarbiyya. lyaye su sani cewa Allah Ta'ala zai tambaye su ranar lahira kan tarbiyyar ya'yansu kuma wallahi in ba su sauke wannan nauyin ba, za su ganu da matsananciyar azaba a jahannama.

**8. Yin faɗa a gaban ‘ya’ya**

Waɗansu iyayen sai su yi ta kace-nace da hayaniya a gaban‘ya’yansu wani lokaci har da zage-zage da doke-doke, wannan ba ƙaramin tasiri yake da shi ba wajen rusa tarbiyyar 'ya’ya.

Waɗannan kaɗan ne daga cikin katafilun da suke rushe duk wani gini na tarbiyya da aka yi. Nan gaba in sha Allah za a faɗaɗa bayanai a kan tarbiyya a cikin maƙaloli da za a rubuta a kan tarbiyya.

Ya Allah ka ba mu zuri'a managarciya ka ba mu ikon gyara

halayenmu. Amin Na gode,

Naku mai buƙatar addu'arku ta gari

Shehu Usman Abubakar

(Shehu Mansur Dala)

12/04/1441 09/12/2019

***********

WAƊANSU DAGA CIKIN

LITTATAFAN DA NA DUBA

Tuhfatul Maudud bi ahkamil maulud-ibnul Ƙayyim

Muhammad ibn Abi Bakar Rahimahullah

Almaktabatul lImiyya Bairut Labanon -1998.

Aubd Dakta

Mas'uliyyatul Aaba'i Tujahal

Abdurrab Nawwabud Din Al-Nawwab Saudiyya

Wizaratusshu'unul Islamiyya.

2-

Attaksir fi Tarbiyyatul Aulad Muhammad bin

lbrahim Al- Hamad

Garkawi Kaduna.

3-

Adam Yunus Masallacin

4

Dalilul Aaba'i Litanmiyati maharatil abna'i

Zakiyyu Mahdi Muhammad Arriba'i - Daru Ibn

Hazm Bairut Labanon 1424/2008.

Fathul Karim bi ahkamil hamil wal janin

Yusif Al- Azzazi - Daru Ibnul Jauzi Alkalhira

1427/2006.

5

-Adil

.